# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN GARIN ZINYAU





*Tsarawar*

Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)



CITAD

*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*

## ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org) is a capacity building Civil Society Organization whose activities covers Research, Advocacy, Training and Publicity in all areas of ICTs.
Its vision is; a Knowledge-based Democratic Society free of Hunger while its Mission is; Using ICTs to Empower Citizens for a just and knowledge-based Society that is anchored on sustainable and balanced development.


**MAIN OFFICE:**

3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria. GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467 • E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org, Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng

**BAUCHI OFFICE:**

NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House, Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312


CITAD | actionaid | UKaid from the British people

# ABUBUWAN DA KE CIKI


Jadawali....i
Godiya....ii
Gabatarwa....1
Manufa....2
Tsarin da aka yi amfani da shi....2-5
Tarihin Garin Zinyau....5-6
Taswirar Garin Zinyau....6-8
Yanayin Zamantakewa....9
Harkar Lafiya....10
Ilimi....10
Juyawar Yanayi....11-15
Kadarori....16
Tantance Haɗɗura....16-17
Tantance Haƙƙoƙin Mata....18
Teburin Lissafin Haƙƙin Mata....19-20
Kalubale....21-23
Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli....23-25
Waɗanda zasu iya Tallafawa....25-26
Cibiyoyi....26
Tantance Yanayin Karfin iko....26
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Garin Zinyau....27
Tantance Hanyoyin Samun Bayanai....28-29
Tsarin da Za abi....30

# GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Gari na Zinyau da Mai Gari da Dagaci da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.





# GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan Gari yana ɗauke da gabaɗayan bayanai filla-filla da kuma taƙaitattun abubuwan da suka shafi GarinZinyau da ke ƙaramar hukumar Rano a jihar Kano a tarayyar Najeriya. Wannan kundi zai zama wani makami na yin wuƙar-ƙugu wajen tabbatar da gaskiyar al'amura ga jama'ar Zinyau. Kundin yayi cikakken bayanin garin da mutanensa da kuma albarkatun ƙasa da Allah Ya huwace masa. An tattaro waɗannan bayanai ne daga wajen wasu keɓantattun mutane mazauna garin ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya domin yin bitar abubuwan da suka gudana da kuma tsarin nan na Action Aid wanda ke baiwa kowa damar bayar da gudummawa don tattara faɗakar da mutane sanin muhimmancin kowa ya shiga a dama da shi a al'amuran zaɓe wanda aka fi sani da (SCEEP).

Tsarin zai zama wani ginshiƙi na aiki tare da wasu garuruwan a ƙoƙarin saita al'umma kan gwadaben da za su rinƙa bibiyar abubuwan da gwamnatoci da wakilansu ke gudanarwa. Haka kuma, wannan kundin zai samar da wata kafa ta yin aiki tare tsakanin al'ummar garin da waɗanda suka zaɓa zuwa matakai daban-daban. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya.

Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike kamar binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa garin barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar garin ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a sama, ActionAid ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a unguwar. Ta amfani da sassa bakwai na tsarin tantancewar bayanai. Bayanan da aka tattara za su zama ginshiƙi na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da garin gaba yadda ake buƙata.

## MANUFA

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gano tare da a dana al'amuran da suka shafi Garin Zinyau tare da fitar da wani tsari na shigo da al'ummar yankin don yin aiki tare.
- Zaburar da al'umma wajen neman abubuwan ci gaban garin daga wakilansu a ɓangarori daban-daban.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da garin Zinyau ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

## HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan garin Zinyau da CITAD.
- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen na garin na tsawon kwanaki domin samun cikakkun bayanai na ɓangarori bakwai na wai waye adon tafiya (Reflection Action).
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

## TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

- An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori bakwai na wai waye adon tafiya (Reflection Action).
- An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabar garin.
- An yi amfani da jerin gwanon haƙƙoƙi ɗan'adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar garin na Zinyau.
- Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar garin suka gano.





- An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.
- An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iya bayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da garin ke buƙata.
- An yi amfani da tsarin zane na Venn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da garin.
- An yi amfani da salon yanar-gizo wajen tantance haƙƙin mata.
- Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da garin.
- Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar garin ke isar da saƙo tsakaninsu da tsakaninsu da sauran garuruwa da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, an tattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

## CIKAKKEN BAYANI GAME DA GARIN ZINYAU

| | |
|---|---|
| Sunan Garin: | Zinyau |
| Karamar Hukuma: | Rano |
| Jiha: | Kano |
| Adadin Al'umma: | 4,700 (A Kiyasi) (Maza 2,200 Mata 2,500) |

Ajujuwan Shekarun Al'ummar Garin
Shekara 0 zuwa 5: 503
Shekara 6 zuwa 10: 397
Shekara 11 zuwa 18: 1,415
Shekara 19 zuwa 30: 830
Shekara 31 zuwa 40: 555
Shekara 41 zuwa 50: 400
Shekara 51 zuwa 60: 410
Shekara 61 zuwa 70: 103
Shekara 70 zuwa Sama: 87
Aikin yi: Noma da Kananan yan kasuwa
Kayayyakin da aka fi sayarwa: kayayyakin amfanin gida, kayayyakin masarufi da sauran kayayyakin sayarwa

Kuɗaɗen da ke shigowa/Kuɗaɗen da ake kashewa
Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: ₦220, 000
Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara: ₦380, 000
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a kullum: ₦390, 000
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a shekara: ₦460, 000

## LALIYA
Garin na da ƙaramin asibiti guda ɗaya wanda ke da tazarar kilomita 6 daga garin, tsahon tafiyar awa 2.






## ILIMI
Makarantu: Garin na da Makarantar Firamare guda 1

| | | | |
|---|---|---|---|
| Adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu: 68 | Adadin Yara Maza: 24 | Adadin Yara Mata: 44 | Adadin 'yan ƙasa da shekara 5: 13 |
| | Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 10: 21 | Adadin 'yan shekaru 11 zuwa 15: 25 | Adadin 'yan shekaru 16 zuwa 20 (idan ana buƙata): 09 |
| Adadin waɗanda suka kammala Firamare: 487 | | | Adadin Maza: 369 |
| | | | Adadin Mata: 118 |
| Adadin waɗanda suka kammala Sakandare a garin: 298 | | | Adadin Maza: 291 |
| | | | Adadin Mata: 007 |
| Adadin waɗanda suka kammala Makarantar gaba da Sakandare: 18 | | | Adadin Maza: 18 |
| | | | Adadin Mata: 00 |
| Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa Makaranta ba: 1,325 | | | Adadin Maza: 908 |
| | | | Adadin Mata: 417 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa Makarantar Firamare: 1002 | | | Adadin Maza: 700 |
| | | | Adadin Mata: 302 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa Makarantar Sakandare: 634 | | | Adadin Maza: 218 |
| | | | Adadin Mata: 416 |

Masu Buƙata ta Musamman: 37 yawanci masu buƙata ta musamman ɗin basu zama a garin su kan tafi garuruwa da ke kusa da garin don gudanar da Sana'o'insu daban daban.




## TARIHIN GARIN ZINYAU

Zinyau ƙaramin gari ne idan an kwatanta shi da garin Rano da ke da cigaba saboda shahararrun ma'aikatan gwamnati da yan kasuwa da ke da su. Cikin shahararrun mutane akawai Alh. Zubairu Zinyau. Zinyau na da tazarar kilomita bakwai daga ƙaramar hukumar Rano a jihar Kano. Garin na arewa maso yamma da Rano kuma na da adadin al'umma da yakai 4700.

Sana'ar noma ita ce sana'ar da tafi shahara ga al'ummar garin, duk da cewa babu makarantar firamare ko ɗaya a cikin garin mutanen garin kan daure wajen zuwa makarantar firamaren da ke Gidan Murabus wani ƙauye da ke kusa kan hanyar Rurum zuwa Rano, kwatankwacin tafiyar kilomita 3. Babu wata cibiyar lafiya da mutanen garin ke zuwa a garin, mutanen garin kan tafi zuwa babban asibitin garin Rano kan duk abin daya shafi lafiyarsu.

Titin daya haɗa garin da babban titi a lalace yake korai da gaske wanda hakan kan jawo wahalar zirga-zirgar ababan hawa.

Zinyau na da ingantattun hanyoyin samun ruwan sha na Rijiyoyin da aka gina a gidaje da gurare keɓantattu a cikin garin.

## TASWIRAR GARIN ZINYAU


An fara fitar da taswirar garin ne ba tare da sanya wata alama ba sakamakon ruwan Sama a lokacin. Amma duk da haka an gano ma'adinai da ƙalubale da matsaloli iri-iri da ke addabarsa domin a ƙarfafi gwiwar al'umma su tattaunawa sosai domin samun mafita. A lokacin aikin, an gano albarkar ɗan'Adam da Allah Ya yi wa yankin da ma'adinai da abubuwan da kan sa walwalar al'umma da kuma harkokin da ake aiwatarwa cikin garin.


Kasar noma na daga cikin albarkatun ƙasa da Allah ya horewa jama'ar garin, garin nada makarantar firamare ɗaya da gwamnati ta gina. makarantar nada dalibai maza da mata. Garin Zinyau gari ne da jama'ar garin baki ɗayan su musulmi ne wanda keda gini masallatai da dama. Garin ya dogara kacokan akan noma, inda yake da tarin gonaki masu yawa. Bugu da ƙari, ga yunkurin gwamnatin jiha na ganin an yi noman kwakwar manja mai yawa a garin na zamani domin sayarwa. Akan yi noman masara, rogo, fasadabur, doya, tattasai, wake da kuma gero.






Garin na da kasuwa guda ɗaya wadda rashin kyan hanya yasa bata ci yadda yakamata. Babu asibiti a garin. Garin Zinyau na da cibiyoyi da ɗakunan taro da mutanen garin ke haɗuwa. Taswirar da ke tafe ta zayyana albarkatun ƙasar da Allah ya horewa garin. Haka kuma ta nuna Karin ababan more rayuwar da mutanen garin ke burin cimma a gaba.














Al'ummar Garin Zinyau tare da Tasawirar Garin



## YANAYIN ZAMANTAKEWA

Zinyau ƙaramin ƙyauye ne da ke da yawan al'ummar da suka kai 4,700 (2,200 Maza da 2,500 Mata). Babu wata ƙididdiga da ta nuna akwai rabe-raben shugabanci a yankin. Akwai mutane 'yan shekaru 0 zuwa 5 masu tarin yawa (domin ƙarin bayani, a duba shafin da akayi bayanin haka a baya).

Har ila yau, mafi yawan jama'ar garin manoma ne da ƙalilan din ma'aikatan gwamnati wanda kowane magidanci yana samun aƙalla Naira N220,000 a shekara sannan yakan kashe kimanin N390,000 a shekara (a ƙiyasin albashin ma'aikata). Mutane sun mallaki rumfunan kasuwanci a garin . Jama'ar garin sukan kashe matsakaicin abin da suke da shi. Haka kuma, garin nada masu ƙananan sana'o'i waɗanda suke samun tsakanin Naira 1,200 zuwa 1,800 a rana




## LAFIYA

Garin Zinyau bashi da cibiyar kula da lafiya ko da ɗakin karbar haihuwa. Jama'ar garin kan tafi babban asibitin garin Rano akan duk abin da ya shafi lafiyarsu. Wasu shekaru da suka wuce garin na Zinyau ya taɓa fuskantar annoba da dama kamar annobar kwalara, maleriya, tifod da cutar gudawa, hakan ya afku ne sakamakon yanayi na rashin tsaftar muhalli. Duk da cewa garin na kusa da Rano, gari na ƙarancin kayayyakin kula da lafiya da za su magance ƙalubalen lafiya a matakin farko. Garin na da ungozomomi yan kaɗan masu kula da haihuwa waɗanda suka taba samun horo, waɗanda suke taimakawa wajen rage matsalolin da ke addabar al'umma dangane da ƙaracin kayayyakin kula da lafiya a garin. Wannan yanayin na garin Zinyau yasa dattawan garin keda shirin tuntubar gwamnati domin ta samar da ɗakin shan magani a garin.



## ILIMI

Makarantar na da ƙarancin ajujuwa sannan kuma babu makarantar sikandire a garin. Akwai buƙatar ƙarin ajujuwa a firamaren idan aka kwatanta da makarantar dake cikin garin Rano. Hakan nan akwai makarantar Islamiyya guda ɗaya a garin wadda kansila ya gina. Domin tantance ingancin ilimi a Zinyau, an yi amfani da kundin da yake ɗauke da hakkokin ciyar da ɗalibi gaba (Promoting Rights in School Charter). Haƙƙin ciyar da ilimi gaba a makarantu ya ta'allaƙa kan haƙƙoƙi guda goma da aka rairayo daga Tsarin Shari'a na ƙasa (National Legal Instruments) (watau kamar kundin tsarin mulki da yarjejeniyar haƙƙoƙin ɗan'Adam na ƙasa da ƙasa).

An yi amfani da shirin PRS domin tantance haƙƙoƙin ilimi a garin. Manufar da PRS ke son ya cimma ita ce shigo da al'ummar ƙasa domin tabbatar da ilimi mai inganci sannan a gane fahimtar 'yan ƙasa a wuraren da suke rayuwa inda A tsarin, lamba 1 ce mafi karanci, 5 kuma lamba mafi girma. Ga haƙƙoƙin:



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN ZINYAU 2016

| S/N | Yarjejeniyar PRS | Tantancewa (1 mafi ƙaranci, 5 mafi girma) |
|---|---|---|
| 1. | Haƙƙin samun kyakkyawan ilimi kuma kyauta | 4 |
| 2. | Haƙƙin rashin nuna wariya | 3 |
| 3. | Haƙƙin samar da isassun kayayyakin more rayuwa | 5 |
| 4. | Haƙƙin samar da wajen zama mara haɗari | 5 |
| 5. | Haƙƙin samar da ƙwararrun malamai | 3 |
| 6. | Haƙƙin samar da tsarin koyarwar da ya dace | 2 |
| 7. | Haƙƙin sanin 'yancin kai | 4 |
| 8. | Haƙƙin a dama da mutum a wajen ɗaukar mataki | 5 |
| 9. | Haƙƙin samar da makaranta mara ƙunbiya-ƙunbiya | 2 |
| 10. | Haƙƙin samar da ingantacciyar koyarwa | 5 |

Jadawali na sama yana nuni da cewa yara ba sa shiga a dama da su a wajen ƙaukar mataki kan wani abu da ya shafi al'umma. Haka kuma samun isassun kayayyakin more rayuwa, sannan ga tauye musu haƙƙi na samun ingantacce kuma kyakkyawan ilimi kyauta da kuma haƙƙin samar musu da ingantacciyar koyarwa.

## JUYAWAR YANAYIN

Garin Zinyau na da yanayi iri biyu; rani da damina. Ana samun yanayin rani ne daga Disamba zuwa Yuni. Damina kuwa tana farawa daga watan Mayu, inda ruwa yakan kankama tsakanin Agusta da Satumba. Jihar Kano kacokan ta fi samun yanayin zafi da yawa, ruwan sama (watau damina) yawanci akan same shi ne a watannin Mayu da Yuni da Yuli da Agusta da kuma Satumba. Kano na samun rani a watannin Janairu da Fabrairu da Agusta. Akan samu matsakaicin zafi a watan Afrilu, yayin da sanyi ya fi tsananta a watan Agusta. Satumba shi ne watan da aka fi samun ruwan sama, haka kuma Janairu ne watan da rani ya fi ƙamari. Ayyukan noma a garin ba shi da yawa sosai sannan kuma ba na kasuwanci ba ne. Mutane a Zinyau suna fara shirye-shiryen shuka a tsakanin Fabrairu da Maris. Jadawalin da ke biye yana nuna yadda yanayin ya karkasu da kuma yadda ayyukan suke gudana a tsakanin waɗannan lokutan.

# YANAYIN ZINYAU A TSAWON SHEKARA

| S/N | Season | Jan. | Fab. | Mar. | Apr. | May | Jun | Jul | Aug. | Spt. | Oct. | Nov. | Dec. |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1. | Noma | L | L | L | M | M | H | H | H | H | L | L | L |
| 2. | Kiwo | L | L | L | M | M | H | H | H | H | L | L | L |
| 3. | Bikin Juyabai | L | L | L | L | L | L | L | L | L | L | H | H |
| 4. | Rikicin Manoma da Makiyaya | L | L | L | L | L | L | L | L | L | H | H | L |
| 5. | Kyanda | L | L | L | H | H | H | H | L | L | L | L | L |

## JADAWALI AYYUKAN MAZAN GARIN ZINYAU NA YAU DA KULLUN

| LOKACI | AIKI |
|---|---|
| 5:00 zuwa 8:00 na safe | Lokacin sallah, Karin kumallo, wanka, gaishe da iyaye, ziyara, halartar bikin raɗin suna ko bikin aure idan akwai |
| 8:00 na safe zuwa 1:00 na rana | Noma, zuwa wajen sana'o'i, kiwo da ayyuka a ma'aikatu daban daban na Gwamnati |
| 1:00 na rana zuwa 4:00 na yamma | Halartar Salloli, abincin rana da kuma halartar sallar yamma |
| 4:00 zuwa 6:00 na yamma | Noma, wasan kwallon ƙafa, zuwa Islamiyoyi, kallo, debo ruwa, samun itacen girki da kuma halartar taron tattauna al'amuran al'umma idan akwai ɓukatar tattauna wani lamari |
| 6:00 na yamma zuwa 10:00 na dare | Halartar sallar magriba, cin abincin dare, saurarar labarai, halartar guraren bada karatu na addini da tattaunawa, kallon gasar wasannin ƙwallon ƙafa da zuwa neman aure. |
| 10:00 na dare zuwa 05:00 na asuba | Lokacin bacci |



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN ZINYAU 2016

## JADAWALI AYYUKAN MATAN GARIN ZINYAU NA NA YAU DA KULLUN

| LOKACI | AIKI |
|---|---|
| 5:00 zuwa 5:30 na safe | Lokacin Sallah |
| 5:30 na safe zuwa 8:00 na rana | (Gyaran gida ) wanke-wanke, shara, shirya Karin kumallo, shirya yara zuwa makaranta da guraren sana'o'i |
| 8:00 na rana zuwa 12:00 na Yamma | Wanki, waɗansu sukan kwanta su huta wasu kuma sukan karanta litattafan Hausa |
| 12:00 zuwa 2:00 na Yamma | Shirya abincin rana, sallar azahar, da kuma cin abincin rana. |
| 2:30 na yamma zuwa 40:00 na Yamma | Baiwa yaran gida abinci sai kuma kaisu islamiyya |
| 40:00 na dare zuwa 6:00 na Yamma | Share gida da kuma sallar la'asar |
| 6:00 zuwa 7:00 na Yamma | Shirya abincin dare da kuma yin wanka |
| 7:00 zuwa 10:00 na Dare | Duba ayyukan gida da aka bawa yara a makaranta, wasu kuma su tafi yin waɗansu aikace-aikacen, halartar sallar magriba da isha, kallon fina-finai domin nishadi |
| 10:00 na dare | Lokacin bacci |

# JADAWALI AYYUKAN YAN MATAN GARIN ZINYAU NA YAU DA KULLUN

| LOKACI | AIKI |
|---|---|
| 5:00 zuwa 8:00 na Safe | Sallah da gaida iyaye da kakanni, zuwa makarantun allo, Karin kumallon safe, wanka da daukan talla. |
| 8:00 na safe zuwa 1:00 na Rana | Halartar makarantun islamiyya,wasu kuma su tafi talla, wasu kuma su tafi gona domin yiwo ciyawa |
| 1:00 na rana zuwa 2:00 na Rana | Halartar sallar azahar da cin abincin rana, zuwa makarantun islamiyya, zuwa kasuwa, sharar gida da taimakon iyaye ayyukan gida |
| 2:00 zuwa 4:00 na Yamma | Sallah, yin wanka, taimakon iyaye aikin gida da zuwa kasuwa cefane. |
| 4:00 na Yamma zuwa 6:00 na Yamma | Zuwa makarantun islamiyya , talla, wasa da kuma taimakon iyaye yin girki da gyaran gida |
| 6:00 na Dare zuwa 10:00 na Asuba | Sallolin yamma, cin abincin dare, halartar islamiyoyi, wasu kuma su tafi wasanni. |
| 10:00 na Dare zuwa 6:00 na safe | Lokacin bacci |




KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN ZINYAU 2016



Jadawali Ayyukan Maza, Mata da Kanana



Yaran Garin Zinyau Na Yau Da Kullun




## KADARORI

Kowane mazaunin garin Zinyau na da 'yancin mallakar gona shanu da gidaje.




TANTANCE HAKKOKIN MATA


'Yancin mata shi ne haƙƙoƙin aka keɓe musamman domin mata da 'yanmata a ƙasashen duniya masu yawa. A wasu wuraren, ire-iren waɗannan haƙƙoƙi an tabbatar da su ta hanyar yi musu doka da tsarin zamantakewar al'umma. A wasu wuraren kuwa, a iya cewa an yi watsi da su. Lamuran da ake dangantawa da haƙƙin mata ba a taƙaita su ga 'yancin yin zaɓe ko taƙaita haihuwa ba kaɗai.


A Arewacin Najeriya, inda garin Zinyau yake, al'ada da addini suna ci gaba da taka muhimmiyar rawa a sha'anin 'yancin mata. An samu cigaba sosai a 'yancin mata musamman wajen faɗaɗa tattalin arziƙinsu da samun damar yin ilimi da kuma yadda suke shiga a dama da su a al'amuran al'umma. Duk da wannan ci gaban da aka samu, har yanzu akwai ƙalubale wajen sanya su cikin al'amuran shugabancin da jin ta bakinsu yayin a ɗaukar wata matsaya kan wani al'amari da ba su muƙamai da kuma ba su damar bayar da irin tasu gudummawar a al'amuran al'umma.

A garin Zinyau, ba ataƙaice yanci samun ilimin mata ba, ana ƙarfafa musu gwiwa su shiga makaranta. Har yanzu akwai adadi mai yawa na matan da aka cire daga makaranta a dalilin za a yi musu auren wuri da sauran dalilai na gazawar iyaye wajen ɗaukar nauyin karatun nasu da makamanta haka. An yi amfani tsarin na cobweb domin a nitsa sosai wajen tantance haƙƙoƙin mata. Aikin yana so ya auna yanayin zamantakewa da tattalin arziƙi da kuma siyasa domin a gano abubuwan da ke kawo tarnaƙi ga ci gaban mata ta yin amfani da abubuwa daban-daban a kan ma'auni na 1 zuwa 5; lamba 5 mafi girma, yayin da lamba1 kuma mafi ƙaranci.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN ZINYAU 2016



## Ma'aunin Cobweb na Maza da Mata

| Ɓangare | Sakamako (Mata) | Sakamako (Maza |
|---|---|---|
| Shugabanci | 1 | 1 |
| Samun kuɗin shiga | 2 | 2 |
| Kula da gida | 1 | 1 |
| Mallakar Kadarori | 4 | 4 |
| Tsaro | 5 | 5 |
| Samun damar ilimi | | 1 |
| Ɗaukar matsaya a al'amuran al'umma | 1 | 1 |
| Damar samun iko | 5 | 3 |
| Shiga Al'amuran Al'umma | 1 | 1 |
| Aikin yi | 1 | 1 |

Jadawalin na nuna tazarar da ke tsakanin maza da mata a lokacin aikin tantance haƙƙin mata. Abin sha'awa, akwai daidaito na kurkusa a ratar da aka samu a tsakaninsu, wanda yake nuna cewa al'ummar garin sun fahimci banbancin da ke tsakanin maza da mata.

A Zinyau, mata ba sa taka kowace irin rawa a fannin shugabanci da shiga a dama da su cikin al'amuran jama'a. Amma duk da wannan, matan yankin suna da kazar-kazar duk da cewa ƙalilan ne ke shiga harkokin ɗaukar wata matsaya da ta shafi al'umma. Suna da 'yancin bayar da gudummawa a al'amuran tattalin arziƙi, amma ban da na siyasa. An amince da cewa mata suna da haƙƙin samun ilimi, amma ayyukansu sun fi ga kula da gida.







Matan Garin Zinyau Yayin Tantance Haƙƙoƙin Mata




Take Haƙƙoƙin Mata

An lissafa haƙƙoƙi ne domin a gano yadda ake tauye 'yancin jama'a a garin Zinyau. An hana al'ummar Zinyau waɗannan haƙƙoƙi:

- Haƙƙin ingantaccen ilimi
- Haƙƙin ingantattun ababen more rayuwa (Lafiya)
- Haƙƙin ingantattun ababen more rayuwa (Ruwa)
- Haƙƙin jin daɗin zamantakewa (Rashin aikin yi)

Take waɗannan haƙƙoƙi ya taimaka ƙwarai da gaske tauyewa tare da rage yin rayuwa mai inganci a yankin. Rashin ingantacce ilimi shi ma wani ƙalubale ne sakamakon rashin ƙwararrun malamai da ƙarancin kayayyakin koyo da koyarwa a makarantu.

| LRP JIHA | KANO | | | KARAMAR HUKUMA | KABO | | GARI | | GAMMO | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | Adadin waɗanda suka cancanci su samu a yankin da akayi shirin | | Al'amari | Abubuwan da suka haddasa | Haƙƙoƙin da aka tauye | Kundin tsarin mulki/ policy enterta -inment | Adadin waɗanda suka cancanci su samu damar da suke neman haƙƙinsu a farkon fara shirin | | Waɗanda nauyin yin aikin ya hau kansu | Sauran muhimman masu ruwa da tsaki |
| | Namiji | Mata | | | | | Namiji | Mata | | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 2,200 | 2,500 | Hanya | Rashin ingantaccen shugabanci | Abubuwan more rayuwa | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 2,200 | 2,500 | - ƙaramar hukumar Rano<br>- Ma'aikatar Ayyuka da Gidaje ta Jihar Kano | Kwamishinan ma'aikatar ayyuka da gidaje<br>• ƙungiyoyi masu zaman kansu |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 2,200 | 2,500 | lafiya | Rashin ingantaccen shugabanci | Haƙƙin samun ingantacciyar rayuwa | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 2,200 | 2,500 | - ƙaramar hukumar Rano<br>- Ma'aikatar Lafiya ta Jihar Kano<br>- Sashin Ma'aikatar Lafiya | Kwamishinan lafiya<br>• ƙungiyoyi masu zaman kansu |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 2,200 | 2,500 | Masallacin Juma'a | Rashin ingantaccen Cigaba | Rashin ingantaccen ababan more rayuwa | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 2,200 | 2,500 | -Hizba ta Kano<br>-Al'ummar gari | • Masu taimakawa al'umma |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 2,200 | 2,500 | Ilimi<br><br>Rashin aikin yi | Rashin ingantaccen shugabanci<br><br>Rashin ingantaccen ilimi | Haƙƙin samun ingantaccen Ilimi Ababan more rayuw | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 2,200 | 2,500 | - Karamar Hukumar Rano<br>- Ma'aikatar Ilimi ta Jihar Kano<br>- Hukumar makarantun Sikandire KSSSMB<br>- Hukumar Ilimi ta bai daya SUBEB<br>-Karamar Hukumar Rano<br>-Ma'aikatar ayyuka da Gidaje | -Kwamishinan Ilimi na Jihar Kano<br>- ƙungiyoyi masu zaman kansu<br><br>Kamfaninnika ƙungiyoyi masu zaman kansu |






# KALUBALEN DA KE FUSKANTAR GARIN ZINYAU A HALIN YANZU

A fili take cewa babu wata al'umma da zata rayu ba tare da ƙalubale ba. Haka shima garin Zinyau na fuskantar wasu manyan ƙalubale guda biyu. Kalubalen kuwa sun dangacin ilimi da ɗakunan shan magani. Waɗannan matsalolin sun samu ne saboda rashin kyakykyawan shugabanci. Haka nan kuma akwai ƙarancin fadakarwa ta ɓarin iyaye da al'ummar garin.

## Sassauƙar Hanyar Jera Matsaloli

| Lamba | Al'amari (Buƙatu) | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYI |
|---|---|---|---|---|---|---|
| **1.** | Hanya | 89 | 35 | 114 | 238 | **Na 1** |
| **2.** | Lafiya | 30 | 01 | 15 | 46 | **Na 3** |
| **3.** | Masallacin Juma'a | 17 | 05 | 49 | 71 | **Na 2** |
| **4.** | Wutar lantarki | 07 | 01 | 09 | 17 | **Na 6** |
| **5.** | Ilimi | 19 | 01 | 06 | 26 | **Na 4** |
| **6.** | Aikin yi | 0 | 0 | 21 | 21 | **Na 5** |







Al'ummar ZinyauYayin Fitar da Sassauqar Hanyar Jera Matsaloli




KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN ZINYAU 2016



# TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI

Bishiyar matsaloli ta taimaka wajen tantance manyan matsalolin da ke addabar garin. Bishiyar hoto ne da ke nuna dangantaka tsakanin abubuwan da suka haddasa matsalolin da kuma tasirinsu. Bishiyar matsaloli tana buɗe ƙofar shiga tsakani tun daga tushen abubuwan da suka janyo ta da zummar warwarewa. Gangar jikin matsalar, kamar yadda aka nuna, ita ce Ilimi (ƙarancin kayayyakin koyo da koyarwa da rashin ƙwararrun malamai da kuma buƙatar ƙarin samun makarantu). Abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu, kamar yadda aka tattauna da al'ummar Zinyau, an nuna a bishiyar matsaloli da ke biye.

Abubuwan da suka taso daga bishiyar matsaloli, an yi nazarin ƙungiyoyi da mutanen da za su iya bayar da gudummawa wajen warware matsaloli. Al'ummar Zinyau sun fitar da muhimman mutanen da suke da zarafin tallafawa domin samar da canjin da ake fata a garin.








| Abubuwan da aka Gano | Waɗanda za su Iya Tallafawa | Cibiyoyi | Manyan buƙatu/ zaburarwa domin kawo canji | Matakin ƙarfin ikon kawo canji ( sosai, tsaka-tsaki ko na-ƙasa) |
|---|---|---|---|---|
| Hanya | 1. Dagaci<br>2. A.Zubairu Zinyau<br>3. A.Sale zinyau<br>4. A. Dantata<br>5. A.Yahuza<br>6. Abdulhadi Usman<br>7. A. Rabiu Tai Tai<br>8. Shugaban Karamar Hukumar Rano<br>9.Kakakin Majalisar Jiha<br>10. A. Garba Bezawa<br>11. Dan Majalisar Wakilai<br>12.Sanata<br>13 Kwamishinan Kananan Hukumomi<br>14. Kwamishinan Lafiya<br>15 .Babban Limamin Zinyzu | 1.Majalisar Karamar Hukumar Rano<br>2. Ma'aikatar Lafiya<br>3. Ma'aikatar Ayyuka da Gidaje<br>4. Ma'aikatar Raya Karkara da Birane<br>5. ma'aikatar Kananan Hukumomi<br>6. Kwamitin Lafiya na Majalisar Jiha<br>7. Kwamitin Ayyuka da Gidaje na Jiha | 1. Cigaba<br>2,Cigaba<br>3.Na Cigaba<br>4.Siyasa<br>5.Cigaba<br>6.Na cigaba<br>7. Siyasa<br>8.Siyasa<br>9. Siyasa<br>10. Na cigaba<br>11.Siyasa<br>12.Siyasa<br>13.Siyasa<br>14.Siyasa<br>15. Na cigaba | 1.tsaka-tsaki<br>2. tsaka-tsaki<br>3. tsaka-tsaki<br>4. tsaka-tsaki<br>5. Na kasa<br>6.Na kasa<br>7. tsaka-tsaki<br>8. Sosai<br>9. Sosai<br>10. tsaka-tsaki<br>11. Sosai<br>12. Sosai<br>13. Sosai<br>14. Sosai<br>15. Sosai |
| Masallacin Juma'a | | | | |
| Lafiya | | | | |

Waɗanda za su iya tallafawa
Bayan an gano matsalolin hanyoyi da abin daya shafi lafiya da cewa sune manyan kalubalen da ke addabar al'ummar Zinyau, al'ummar yankin sun tattauna game da muhimman mutane da ƙungiyoyin da gudummawarsu za ta iya kai wa ga cimma burin da ake da shi na daga darajar ilimi duba da zaburarwa da matakinsu na kawo canji.

An fitar da masu tallafawa al'umma da shugabannin al'umma da shugaban ƙaramar hukumar Rano da kwamishinan lafiya da ɗan majalisa da masu riƙe da sarautun gargajiya a matsayin muhimman mutanen da ke da ƙumbar susa.

## CIBIYOYI

A matakin hukumomi kuwa, ma'aikatar lafiya, ma'aikatar ayyuka da gidaje da ma'aikatar raya karkara da birane sun taka rawa daban-daban wajen warwaren matsalolin garin. Duba jadawali na sama da ya yi bayani dalla-dalla,




### TANTANCE KARFIN IKO

An yi amfani da tsarin zane na Venn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma an yi amfani da tsarin zanen Venn Domin tantance matakin da wutar lantarkin yake ko ikon da wani mutum ko wata ƙungiyoyi ke da shi da kuma alaƙarsu da juna.

Zanen ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano.

Majalisar Jiha da Kwamitin lafiya na Majalisar suna da tasiri da ƙarfin ikon kawo canji da kuma haɓaka kayayyakin aiki na lafiya ga al'ummar garin. Hakan yana da alaƙa da Ma'aikatar ayyuka a matakin jiha da majalisar karamar hukuma da al'ummar gari. Ma'aikatar lafiya ma tana da tasiri sosai da kuma kyakkyawar alaƙa da Kwamitocin lafiya da na ayyuka a Majalisun Jiha da Tarayya. Ita ma ƙaramar hukuma da Majalisar Jiha suna da kwatankwacin irin wannan tasirin. Haka nan majalisar ƙaramar hukuma tana da kyakykyawar alaƙa tsakanin al'umma da jiha dama majalisin Jihohi da na tarayya.





Dagaci da kansila dammar da suke da ita bata kai ta kawo ba wajen kawo canji duk da cewa suna da alaƙa ta ƙud da ƙud da al'umma da kuma shugaban ƙaramar hukuma. Akwai mutane masu tarin yawa waɗanda suke taimakawa kai tsaye ko ta gefe wajen ciyar da al'umma gaba. Waɗannan mutane na da ɗan tasisri samar da canji kuma suna da alaƙa ta kai tsaye da mambobin majalisar tarayya haka nan kuma suna da alaƙa ta kai tsaye da al'umma.



### TANTANCE MATSALOLIN DA KE ADDABAR GARIN ZINYAU

Tantance matsaloli hanya ce ta gano da auna da kuma jera matsalolin da ke fuskantar garin daki-daki. Bugu da ƙari, An gano matsalolin da ke yiwa garin barazana. An yi amfani da jadawalin tantancewa wajen tattauna sabubban da suka haddasa su tare da tasirinsu.

| Lamba | Matsala | Abin da ya Haddasa | Tasiri | Waɗanda suka fi Cutuwa |
|---|---|---|---|---|
| 1. | Sace-sace | - Rashin aikin yi<br>- Jahilci | -Yana jawo asarar Dukiya | Gabaɗayan Al'umma |


Matsalar sata ita ce matsalar da ta fi addabar jama'ar garin, hakan kuwa ya faru ne saboda matsalolin rashin aikinyi, gaza kamalla karatu, rashin gudanar da aikin jami'an tsaro yadda ya kamata a cikin garin da kuma rashin ingantacciyar manhajar karatu a tsarin karatu daga gurin gwamnati. Matsalar sata da rashin tarbiya a gurin matasa yana jawo mutaƙar koma baya a wannan gari. Matsalolin na faruwa ne yau da kullun musamman a lokacin bukukuwa. Rashin aikin yi shi yake haifar da matsalar sata da kuma ƙarancin tarbiya ta gari daga gurin iyaye da jama'ar gari. Hakan nan matsalar satar ta haifar da ƙalubalen gurɓacewar halayya da asarar rayuka da dukiyoyi da kuma munanan ɗabi'u. An saka matsalar sata a matakin farko saboda al'ummar garin da taimakon yan kato da gora suna ɗaukan matakan shawo kan matsalar.



# TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Manyan hanyoyin samun bayanai a garin Zinyau sun haɗa da radiyo da talabijin da yanar gizo da jaridu da Mujallu da tauraron Ɗan'Adam da shela da wayar tafi-da-gidanka da tattaunawa da kuma tarurruka. A wasu lokutan akan yaɗa bayanai a wuraren raɗin suna ko ɗaurin aure da kuma cibiyoyin addini da ke garin.

Wayar tarho da tattaunawa fuska da fuska hanyoyi ne da al'ummar Zinyau suke isar da saƙonni ga takwarorinsu na wasu garuruwan. Dagaci da masu unguwanni su ne masu magana da yawun al'ummar garin, kuma suna da ƙarfin iko fiye da kansilan da aka zaɓa.










# TSARIN DA ZA ABI

A ƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran tsarin da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar yin amfani da gudummawar kowa da kowa da wasu dabaru domin tantance abubuwan da ke ci wa al'ummar garin Zinyau tuwo a ƙwarya. Abin da ke biye tsari ne na ayyukan da za aiwatar domin ganin mafarkin garin ya zama gaskiya.

| Muhimman Abubuwa | Hanyar da Aka Tsara | Lokaci | Masu yin Aiki | Abubuwan da ake buƙata | Matsaloli | Hujjar Samun Nasara |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Ziyartar wasu Rukunonin Al'umma a Zinyau | Ziyara ta kai tsaye | Sati 2 ( 15 zuwa 30 Disamba 2015) | Kwamitin kundin na Zinyau | • Bayanin shirin<br>• Taswirar Rukunonin Al'umma | • Lokacin kaka | Rahoto |
| Rubutaccen bayani game da CDC | Gabatarwa da karɓar shawarwari | Sati 2 30 ga watan Nuwamba | CITAD da Al'ummar Gari | Rubutaccen bayani game da CDC | Lokaci da kuɗi | Cikakken rubutaccen bayani game da CDC |
| Kaddamarwa | Tattaunawa don tsara shiri | Janairu 2016 | CITAD da Al'ummar Gari | Rubutaccen bayani game da CDC | Lokaci da kuɗi | Kaddamar da kundin CDC |
| Ziyarar ƙarfafa gwiwa ga waɗanda nauyi ya hau kansu | Ziyarar ban Girma da rokon Iri | | CITAD da Al'ummar Gari | Cikakken rubutaccen bayani game da CDC | Bayan ƙaddamarwa Watan Fabrairu 2016 | Sadaukarwa |